# Rediyo: A Duniyar Mu Ta Yau.

**Jawabi a Wajen Bikin Bude Gidan Rediyo Nagarta, Katabu, Mararrabar Jos, Jihar Kaduna, Asabat, 26.2.2005.**

Yusufu Bala Usman,
Ceddert,
Hanwa, Zaria.

Assalamu Alaikum Jama'a. Mun taru ne, yau, domin bikin bude Gidan Rediyo Nagarta, wanda kirarin shi, shi ne, *Muryar Hada Kan Jama'a!* Saboda haka, ya kamata, a wannan biki, mu nemi amsar, a' kalla, tambayoyi biyu.

**Hanyoyin Sadarwa**

Tambaya ta farko, ita ce, shin menene matsayin rediyo a duniyar mu ta yau? Duniyar da, ke da talibijin, mai mamaye ta, gaba dayan ta; ana baza shirye – shirye; daga - safe - har – dare; daga - dare - har safe. Duniyar da ke da injin mai kawakalwa, wanda ya hada duniya duka, ta hanyoyin sadarwa na intanat, a kowane lokaci, kuma har zuwa kowane lungu, a kan kasa, a sararin samaniyya, har ma a duka fadin tekun da ke duniya. Duniyar da ke da wayar salula, wadda, babu sakonni, labarai, hotuna, da zane – zane, da ba za'a iya aikawa ba, cikinta. A takaice, dai, a duniyar da a ke ta mamayewa, da wadannan sababbin hanyoyin sadarwa, menene matsayin wannan tsohuwar hanyar sadarwa ta rediyo?

**Hada Kan Jama'a**

Tambaya ta biyu, ita ce, shin menene ma'anar, hada kan jama'a, da Rediyo Nagarta ke kirari da shi? Shahararren mawakin nan namu, Mallam Abubakar Ladan Zaria, a muhimmiyyar wakar nan ta sa, *Allah, Ya Allah, Ya Allah! Hada Kan Mu Afrika Mu So Juna!* ya ja kunnen mu, ya ce:

*Hada kai ,ba wai hada baki ba.*
*Ai zambo, ko ai cuta ba.*
*Da wulakantar da mutane ba.*
*Ko zalunci da fashin kai ba.*
*Yanci bai yarda da wannan ba.*

*Dukkan fitina daga jahilci, ta ke,*
*Tushe ko na ta,lalaci.*
*Shi ke jawo a yi zalunci.*
*Da matsawa, son karbar hanci.*

*Duka ba wannan a cikin yanci.*

Saboda haka, menene ma'anar hada kan jama'a nan da Rediyo Nagarata ke kirari da shi?

**Bautar da Jama'a**

Hadin kai ne na ya'ya, domin dukkan jama'a su samu yanci da cigaba a rayuwar su? Ko ko, hadin kai ne tsakanin bayi irin na zamani, da ma su bautar da su, su ma irin na zamani, domin a gina ma bauta, tushe, a kara taushe bayi, a duniyar nan ta mu ta yau?

Wato, a yaudari, yawancin jama'a su bi, a gyara ma bauta gindin zama, a yi mata kwaskwarima, a cigaba da ita, domin biyan bukatar masu bautar da jama'a?

Bautar da jama'a ana yi ta ta hanyoyi da dama. Amma muhimman hanyoyin biyu ne. Hanya ta farko ita ce masu mulki, da masu mallakar kaddarori a kasa, su bautar da jama'ar kasar su, da kansu, su taushe kowa, karkashin su.

Hanya ta biyu ita ce, masu mulki a wata kasa, su mamaye wata kasa daban, da yaki, ko da zambar siyasa, ko da dabarun mallake kusoshin tattalin arzikin kasar, su bautar da kasar gaba dayanta, da duka abinda ke cikinta.

**Muhimmancin Rediyo**

To kafin mu gama da wannan batu na ma'anar hada kan jama'a, gwamma mu gama da batun mu na farko, na matsayin rediyo a duniyar mu ta yau.

To a gaskiya dai, duka da cigaban da a ka samu, wajen sadarwa, ta hanyoyin talabijin mai mamaye duniya, da intanat, da wayar salula, har yanzu dai rediyo shi ne muhimmin hanyar da yawancin jama'ar duniya ke samun labarai, ta wayar - iska. Domin shi rediyo, yana da saukin kudin saye da sarrafawa. Yana kara arha, kulli – yaumin. Kuma yana amfani da batir, ba sai da lantarki ba. Talabijin kuwa, da kwamputa, da salula, sun ninka rediyo, ninkin - baninkin, wajen tsada, kuma ba sa yi sai da lantarki, da daure – dauren wayoyi iri – iri.

Banda tsadar sayensu da wahalar sarrafa su, rediyo ya fi su sauki wajen jama'a, domin shi, ba sai ka zauna ka kura mashi ido ba, kana tabe – tabe, kamar su talabijin da kwamputa. Zaka, iya cigaba da aikin noma, ko kiwo, ko sassaka, ko gini, ko wasu sana'oin hannu, kuma kana jin rediyo. Saboda haka har yanzu, a duniyar ta mu ta yau, rediyo shi ne a kan gaba wajen hanoyin watsa labarai ta wayar – iska.

A da, kurtun rediyo sai wane – da – wane. Amma, yanzu yawancin talakawa suna iya sayen rediyo; suna kuma

iya sayen batir din rediyo. Saboda haka a duniyar nan tamu ta yau, daga nan Katabu, a Nijeriya, a Afrika ta Yamma, har Kasar Sin, har India, har Indonesia, har Afrika Ta Kudu, har Brazil, har Bangladesh, har Mexico, har Kasar Masar, babu hanyar watsa labarai, ta wayar iska, da ta kai rediyo muhimmanci. Kuma a nan nahiyoyin mu na Asia, Afrika da Amrika Ta Kudu, uku bisa hudun jama'ar duniya su ke. A nan babu wata shakkar muhimmancin rediyo.

Amma, ko ma a Kasashen Tarayyar Turai, da na Arewacin Amrika, har yanzu rediyo yana nan da muhimmancin, duka da mugun kallon talabijin da su ke yi. Masu nazari da binciken halin rayuwar jama'a sun gano cewa, a kasashen da yawancin jama'a, balle ma yara, su ka dukufa da kallon talibijin, fasahar su, da hankalin su, na dakushewa.

Wato duka wanda ke zura ma talibijin ido, da kunne, awoyi masu yawa, a kowace rana, ya kan sami rauni wajen hankali da fasahar shi, ya rika wasu halaye kamar na butum – butumi, da a ke ce ma *zombie*.Wannan matsala, su ma su mulkin kasashen nan, ba su son a fito da ita fili, a tunkare ta a yi maganin ta, domin rashin hankalin jama'ar, su yana saukake ma su wajen sarrafa su. A ba su abinci mai sa kibar kumburin jiki; a basu kayan kwalliyya wajen wasanni, da wajen biki, kyalkyal banza, su yi ta hidima kan wadannan; su kuma masu mulkin su, su yi amfani da su.

Amma, a kasashen mu, rediyo shi ne kan gaba. Da shi ne a ke wayar da kan jama'a; a yaye ma su jahilci. Da shi ne a ke dawwamar da duhun kan su. Da shi ne a ke a yaudarar su. To, wannan muhimmin matsayin na rediyo a cikin hanyoyin watsa labarai na duniya, me ya jawo mana? Ya jawo mana cigaba, da yanci, da mutunci, da hadin kan jama'ar mu? Idan ya jawo mana wadannan abubuwan alheri a rayuwar mu, to , ta yaya za mu tabbatar sun dore, ba su ruguje ba? Idan bai jawo mana ba, to ta yaya za mu yi amfani da shi rediyo mu same su, mu rike su, mu amfana da su, ya'yanmu da jikokinmu?

**Rufa Ido**

Kafin mu iya tashi tsaye, mu nemo amsar wadannan tambayoyi, sai mun fahinci irin rufa - idon da a ke yi mana a kan tsarin siyasa, mulki, tattalin arziki, da rayuwar jama'a a ko ina cikin duniya. Domin, ko yaushe gwamantocin yan jari – hujja na Amrika da Turai suna ambaton cewa komai su ka yi su na yi ne domin tsare, kuma da inganta mulkin dinmokaradiyya a duniya ba ki dayanta.

Mulkin dimokaradiyya ba wani abu ba ne a dunkule, wanda wasu kasashe ke da shi, wasu kuma ba su da shi. Dimokaradiiya tsari ne na mulki da rayuwar jama'a wanda ya banbanta a kasashe daban – daban na duniya. Kuma dimokaradiyya ba kawai yin zabe ba ne. Wato dimokaradiya ta fi karfin kirgan kuri'a! A tarihin duniya akwai dimokaradiyya kamar hawa uku.

Da farko dai, akwai tsarin dimokaradiyya da a ke kira da turancin Ingilishi, *liberal democracy*, wato tsarin dimokaradiyya wanda ba abinda ya kunsa, sai bikin takarar zabe, da jefa kuri'a, da lissafin kuri'a. Wannan tsari ne da ya tabbatar da mallakar, gonaki, filaye, gidaje, da sauran kaddarorin rayuwar jama'a, a hanun, yan jari – hujja. Jamaa yan kasa, iyaka su jefa kuri'a, su bar ma masu dukiyar kasa,su cigaba da mallakar ta, da sarrafa rayuwar kowa – kowa, ta yadda su ke so.

Daga nan akawi tsarin dimokaradiyya nan wanda a ke kira da turancin Ingilishi, *social democracy*. Wato tsarin dimokaradiyya wanda, ana jefa kuriar zabe, amma kuma ya tabbatar ma dukkan jama'ar kasa hakkokin su wajen rabon arzikin kasa, ta hanyoyin tabbatar kowa ya samu, gwargwadon ruwan sha, ya samu abinci, ya samu kiwon lafiya, ya samu muhalli, ya samu ilmi; ya samu aiki, ko ko, ya samu alawus na rashin samun aiki. A wannan tsarin dimokaradiyya, gwamnatoci na da hannu wajen mallakar gonaki, da filaye da maaikatu, da sauran kaddarori.

A cikin hanyoyin sadarwa irin su BBC, VOA, da CNN da sauransu, wadanda su ke da karfi wajen bayyana ma mutanen kasar nan abinda ke faruwa a duniya, wannan irin tsarin dimokaradiyya ana boye shi. Sai ana nuna cewa a kasashen da su ka cigaba wajen tattalin arziki, zama ne na yan jari hujja zalla, babu wani muhimmin tallafi da gwamnati ke ma jama'a. Ana wannan rufa – ido ne domin kada mutanenmu su ce su ma a yi masu haka, da dukiyar su da gwamanatocin mu suka tattara.

Kamar wajen noma. Duka kasashen da su ka cigaba wajen masana'antu, suna kashe dimbin kudin su wajen ba manoman su tallafi, domin su cigaba da noma, ko - da - riba – ko - ba - riba! A duka kasashen nan ba jama'ar kasar da basu samu aiki ba, alawus na rashin samun aikin yi, domin kada su galabaita da yunwa; ana kuma tabbatar da kiwon lafiyar su da, ilmin 'ya'yan su; a biya da kudin jama'ar kasa da gwamnati ta tattaro. Ba kyauta ba.

Daga nan akwai tsarin da a ke kira, *socialist democracy.* Wannan shi ne tsarin da talakawa na jefa kuria su zabi wanda su ke so, kuma suna mallakar, gonaki, filaye, ma'aikatu, da kaddarori, da sauransu; ba sai yan jari hujja ba, ko sai gwamnati da kan ta. Talakawa na mallakar kaddarorin ne ta hanyoyin, daban – daban. Banda hanyar kowa – da – na - shi; har da hanyar kungiyoyin hada kai na manoma, makiyaya, yan tireda, masu sanao'i. Har ma da kananan hukumomi, da gwamnatocin jihohi, da na kasa baki daya, da jami'oi, da hukumomin bincike – bincike. Da dai hanyoyi mallakar kaddarori iri – iri wadanda su ka yi daidai da, tarihin siyasa da zaman jama'a a kowace kasa.

Cikin wadannan hanyoyin mulki, da sarrafa tattalin arziki, a kan dimokaradiyya guda uku, babu kasar da ke bin daya cikin su, zallar shi. Amma gidajen sadarwa na talibijin da rediyo, da jaridu, da mujalloli na Kasashen Turai da Arewacin Amrika, da ke da karfi a kasashenmu, suna to sheka karya, suna rufa ido, kulli – yaumin, wai, cigaba sai an bi tsarin jari – hujja zallar shi; wai wannan shi ne kadai dimokaradiyya. Alhali kuwa a kasashen su, gwamnatocin su, da yan jari hujjar su, ba su isa su bi shi zallar shi ba. Sai a nan kasashenmu, su ke amfani da kwadayi, da lalacewar shugabanninmu, su na ta puropaganda, suna cusa mana hanyoyin tattalin arziki, da zaman jamma'a da su ke nakasa mu, su wargaza mu, su hargitsa mu, domin su cigaba da danne mu.

**Tsara Gaskiya**

To, ina wannan sabon gidan Rediyon Nagarta ya nufa? Muna fata zai bi tafarkin tsara gaskiya, hada kan jama'a, da kishin kasa. Kada ya zama dan amshin Shata. Ga dai abinda Mallam Abubakar Ladan a wakar shi ta hada kan Afrika, ya gano, kuma ya fayyace mana:

*Kwadayi ke ta da wulakanci.*
*Shi ke cin karfin adalci.*
*Da siyasar nan ta fakiranci.*
*Ka shake cikin ka da zalunci.*
*Me za ka fada a cikin yanci.*

*Sai an manta da su zalunci.*
*An zauna an kashe jahilci.*
*An tunbuke, tushen lalaci.*
*Roko da bara da tumasanci,*
*Na rashin aiki da yawan barci.*

Allah, ya ba masu wannan gidan rediyo, da ma'aikatansa dama, da basirar, da za su yi aiki da abinda wannan sharhi ya kunsa. Amin.

Allah ya kara karfin dankon hadin kan mutanen kasarmu, Nijeriya, da dankon hadin kan duka mutanen nahiyar mu ta Afrika, da duka sauran Bani Adamu da ke neman yanci, adalci, mutunci, da cigaba, tare da kowa – da - kowa, a duniyar nan ta mu ta yau. Amin